# HANZARI!



...lokaci na kurewa!

Zarafi ce ta musamman agare mu domin mu bayyana maka lokaci kiran Allah zuwa ga Ikklisiya. Don Allah ku karanta wannan sako da budden zuciya domin Ruhu Mai Tsarki yayi Magana da ku.

***"Ba ku chewa, Da wata hudu kana girbi ta yi? duba ina che maku, ku tada idanuku, ku duba gonaki, sun rigaya sun yi fari, sun isa girbi"*** ~Yohanna 4:35.

Ugbangiji Yesu Almasihu ya ba Ikklisiya Babbar Umurini, nawaya da zarafin fadawa duniya bishara game da shi, abin da ya kamala domin yan adam su sami rai da yake bayarwa ga dukan wadan da sun zo gare shi. Amma a fili yake kuma, abin takaici ne a gan ikkilisiya ta badda karfin ta akan Ababan da basu da muhimmanci kuma abinda ya kyautu ta yi, bata yi shi ba, wato batun bangaskiya (Markus 16:15-20). Ya yin da ka karanta wannan yar takardan, yana da muhimmanci ka sani cewa duk lokacin da ka yi lumfashi, akwai rayuka da ba za a kidayaba, suna gangarowa cikin wuta jahar-nama da an shirya wa Ibilis da ma' aikatansa har abada abadin. Ko ka tuna da kalmomin yesu acikin markus 16: 15? "ya kuma che masu, ku tafi cikin duniya duka, ku yi wa'azin bishara ga dukan halitta." Babban tambayya agare mu shine: **MENENE KANA YI DA KANKA GAME DA UMURIN UBANGIJIN NAN?** Ya fi zance ka che zaka yi tunani akan batun; tana bukata hanzari! Bukutan wa'azin bishara zuwa battatu abunena hanzari! Muna rayuwa gaban duniya mai mutuwa mai bukatan bishara na mulki. Abin mamaki ne a gan kowa na cewa yana da dangantaka mai kyau da Allah kullayomi amma duk da hakka zamu iya jin bugun zuciyar Allah domin battatu rayuka. Ka yi tunani akan zafi da Allah yana jin a zuciya ya gan wanda ya badda dansa Yesu Almasihu domin ya mutu domin sa ya tafiya zuwa wutar jaharnama. Mun yi tunani yadda zata zafir-ce yesu a zuci ya gan tamanin jininsa daya biya, ya sha wahala domin duka su tsira, ya sake gani wadan nan mutane na lalacewa; musamman wadan da ba su taba jin bishara ba game da rai madawami ko kuwa kubutarwa ta wurin bangaskiya ta wurin yesu Kristi, mutane da dama basu ta ba sami zarafi su ce I ko a'a ga Yesu ba, amma kullayomi suna ga hanya mutuwa na madawami gaba da ra, ayin su. Wanene zaya gayya masu?

## MUTANIN

Da zara mutumiya sami ceto, yana da nawaya ya gan wadan su sun sami ceto, ba gwanintan mutum ba amma aikin Ruhu mai Tsarkine. Mu tsarkaka an bamu amanar kai bishara ga kowa da kowa acikin duniya ya ji abinda Allah yayi ta wurin Dansa yesu Almasihu domin su. Idan ba ka mika kai ga wannan amana ba, koda wane aiki ka ke yi da

matsayin ka, ka dagula abu mafi muhimmanci arayuwa. Allah ya ba wa kowane mai bi Yesu Kristi hidimar sulhu (2Kor 5:18-19). Wannan shine mu na fadi, ba muda dalilin na kowace iri mu ki a-mince da wannan amana. Ba kawai shirin Wa;azi da zamu yi ba amma bishara ne da za mu sanar wa duniya da hanzari misali rai guda a lokaci guda.

Hanzari bishara nan abu ne wadan ba za'ayi wasi da shi ba. Abayyane yake cewa ubangiji yesu bai ji dadin jinkiri da muke nunawa game da Babban umurni da yabamu amana ba. Baya damu da ya-wan ayuka da muke da su a ikklisiya ba, ko yawan zuwa ikklisiya fiyar da Babban umurni da ya bamu ba. Babu abu da zaya canza ra' ayin Allah na gani battatu sun tsira shine yasa ya badda makadacin dansa domin ya cika shirin fansa, ka sani cewa kai ne bege da duniya tana da shi domin ta ji bishara. Kai ne amsar addu'ar Allah: “saboda haka kuyi addu'a ga ubangijin girbi domin ya aiko ma' aikata cikin girbin sa.” (Matta 9:38). Ko abokan ka da makwabtan ka sun ji bisharah yesu Kristi? Allah zai tambaye ka! Idan mutun ya karbe bishara kuma ya ki ya gayyawa, Wadansu, yana nuna a fili halin na sonkai wanda ke gaba da manufar Allahntaka.

## SAKON

Allah ya ba ikklisiya umurnin kai sakon nan ga duniya. Bulus ya furta acikin Romawa 1:16 “Gama bishara ba abin kunya agare ni ba, amma ikon Allah zuwa ga ceton dukan wanda ya baddagaskiya…” Ruhu yana Magana ta wurin Bulus, anan, cewa Bisharan Kristi yana sa ikon Allah ya bayyana cikin aiki domin ceto duk wanda ya badda gaskiya. Saboba haka menene Bisharan Kristi? Wace albishiri ne da ta kawo? Yesu ya bayyana a fili game da kansa acikin Yohanna l0:l0, yace “Barawo baya kan zo ba, sai dai domin ya sata, ya kashe ya hallakar:Amma na zo domin su sami rai, su kuma sami shi a yalwace.” Mun gani Bisharan Kristi yesu shine: Rai madawami ayalwace ga dukan wadan da sun badda gaskiya! Lokaci yayi da” Zamu fadawa duniya cewa ba yesu ne yana sata masu ba, amma ya bayas da albarku ayalwace; ba yesu ne mai kisan kaiba, amma shine mai badda rai. Yesu ba mai hallakaswa ba, amma yana warkas da karyayar zukatar, yana sa rayuwa da an kakarya, ya har-hada ya zuma mai manufa da albarka.

Albishiri shine yesu Kristi ya zo ya canza mutuwa zuwa madawamin rai ga dukan masu bada gaskiya gare shi sun kuma karbe shi, komi yawan zunuban su, za'a gafarta masu a kuma canza su daga mulki mutuwa zuwa rai, daga duhu zuwa haske, daga ikon shaidan zuwa Ikon Allah (Yahaya 5:24; Ayukan Manzani 26:18). Halleluyah! Duniya tana bukata ta ji wannan! Ka taimake duniya ta dandana wannan kamna da Allah uba mai alheri yayi domin su tsira.

## AGABANSA

Babu mutum da zai iya ribato rayuka zuwa ga mulkin Allah da iyawan mutumtaka. Aikin Ruhu mai Tsarki ne yasa Kalmar Allah ta shiga zuciyar mai zunubi ya kuma canza shi. Shi yasa mutane da dama sun kasa yin nasara.Ba su gayyatar Ruhu mai Tsarki cikin aikin ribato rayuka, kuma sakamakon babu nasara. Yesu ya sani ba zamu iya yin kome ta wurin iyawar mu ba, shi ya sa yi alkawalin kasancewa da mu.Yace "… ina tare da ku kullayomi har matukan zamani." (Matt. 28:20). Markus 16:20 yace, "sun tafi ko ina sun yi wa'azi, ubangiji yana aiki tare da su, ya kuma tabatar da kalman ta wurin alamu. Amin" Wannan nassi tana nantawada karfi cewa Allah bai kira mu yi masa aiki ba amma mu yi aiki tare da shi. Wato tarayya cikin aiki na Iyali guda da Allah ke nan wanda a sarari yake cikin 1Korin 6:1, "Mu kuma ma'aikata tare da shi…" Mun gani a cikin Nassosi kasance-wan Ruhu mai Tsarki shine kasancewar Yesu acikin rayuwan mu (Yoh 14:16-18). Kasancewar Allah ne yana bamu karfiribato battatu zuwa ceto. Ruhu mai Tsarki yana son mun yi taraya da shi acikin aikin bishara. Yana bishe mu yadda zamu yi addu'adomin battatu da kuma yin hidimma mai karfi na kalma zuma gare su, ko kuma sakon sulhu. Yana da muhimminci a kullayomi mu gayyace Ruhu mai Tsarki ya taimake mu shaidaYesu kafin mu fita wa'azi, kuma sakamakon zai zama abin mamaki. Ruhu mai Tsarki shine cikaken dabara yadda zai iya sa kowane mutum ya ji wannan sako na daukaka a lebunan mu.

## ADDU'AN

Ko da addu'a ya yi sawo, ko kuwa guntu, babu ma sala, sai dai ya kasance bisa ga hanyar littafi mai Tsarki. Hanyar littafi mai Tsarki yadda zamu tsira an bayyana shi a cikin Romawa 10:9,10, wanda yace" Idan ka furta da bakin ka ubangiji Yesu, ka kuma gaskanta acikin zuciyar ka cewa Allah ya tashe daga mattatu, zaka ka tsira Da zuciya ake badda gaskiya zuwa adalci, da baki ake furta zuwa ga sami Ceto. "Addu'a ta ceto ta kumshi badda gaskiya cikin zuciya mai tuba cewa Allah ya tashe Yesu Kristi daga mattatu DA furtawa da bakinsa cewa Yesu Kristi ne Ubangijin rayuwansa, bayan wannan sai mutum ya sami tsira wani abu fiyed da hakka, bakowace. Mu lura cewa addu'a dole mu mika wa Uba cikin sunar Yesu!

## FALKASWA KO KUMA GIRBIN

Ba manufar Allah bane domin falkaswa ta zama yaren Ikklisiya, amma abin takaici ta zama abin jan hankalin Ikklisiya kullayomi da kadan dakadan. Kalmar nan FALKASWA" na nufi kokarin sa wani abu ya rayu. Sai dai abu mai rai yana bukuta wasakewa (falkaswa). Yana da muhimminci ka amince cewa Allah baya tabba ba mu madawamiyar rai da tana bukata tallafi da koskorima ba, ta

zama cikaken rai wada Allah ya ba mu daidai da nasa kamani (wanda ana kira “zoe” a Helleniyanci). Falkaswa ta shigacikin Ikklisiya a sanadiyar fadiwa ko kuma kasawa domin a daga manufar Ikklisiyan. Manufan ekklisiya ba wai kawai akan ayuka ba amma domin a kai bishara zuwa ga wadan da ke mutuwa cikin zunubi aduniya. Son Allah ne domin ekklisiya ta zama a fadake da kuma araye, ta bar wutar falkaswa tana konowa domin ta yi rayuwa cikin manunfan ta da karfi. Gaskiya ne idan mu yi zabi mun kasance a kusororin hudu na Ikklisiyar mu, domin mu ci gaba da “kange ceton mu” maimakon kai bisara domin ceton duniya mai mutuwa, mu ma da kan mu ba za a jimma ba za mu soma neman ceto da kan mu. Kamata yayi munfita a cikin wurin taruwa a ekklisiya! Gama girbi ya nuna. Duniya bata son falkaswa, suna bukatan girbi, domin sun rigaya sun nuna! Me zaya faru idan aka bar anfannin gona da ya nuna babu girbi? Da gaskiya amfanin zata lalace. Yana da sada sosai a yi kunen shegu da umurnin Allah. Ka tuna idan baka yi biyayya ba Allah ba zaya tambaye ka! Ubangiji yace a cikin Ezekiel 3:18-19.

“Idan na cewa mugu, zaka mutu, kai kuma ba ka fadakar da shi ba, wannan mugu mutun zaya mutu acikin muguntarsa, amma zan bida jiminsa a wuyar ka. Idan ka fadakar da mugun nan sai ya ki ya juyo daga muguntarsa, zaya mutu acikin muguntarsa, amma zaka kubutarda ranka” ba dole ne sai ka bar abinda ka ke yi ka zama Pastor ba, ko kuwa mai bishara kafin Allah yayi amfani da kai ba. Amma dole ka yi bishara ga battatu a masayi da ka sami kanka, ko'ina da Allah ya sanya ka a wurin da ka ke akwai manufan kasancewarka a wurin! Tsarkaka bai rasa abin da zai yi girbi ya gan hasi ta shiga rumbun Ubangiji ba. Muna da Ruhu mai Tsarki; shafewa, furci; juyayi, bangaskiya, wuta Ruhu mai Tsarki da sauran su. Bamu da dalili da zamu jira kuma!

## LOKACIN AIKI

A dukan duniya, bukata Bishara tana da girma, na son amfani da lokaci da kuma hanzari. Bisharan tana cikin hannunka yanzu, menene zaka yi da-shi? Ko zaka yi shelar ta, ko ko zaka boye ta? Idan ba mu zabi kai bishara a saukake ba, a tilasa mu kai ta da matsi (ka duba Ayukan Manzani 1:8,8:1). Ubangiji cikin alherinsa ya zabi ya bayana wannan a tsiri alokaci kamar hakka, dole ka yi hanzari kayi wannan aiki. Da zara muyi jinkiri aiki zata karu da girma a hannun mu. Malaiku ba su ribato rayuka, Uba kuma da Yesu ba za su yi ba, aikin mu ne ta wurin taimakon Ruhu mai Tsarki. Jinkirin mu yana nuna mun yi na' am da Ibilis.mun yadda masa yayi amfani da zarafin domin ya sami Karin lokaci domin ya sata, ya kashe ya kuma hallakar (Wahayin yahaya 12:12; Yahaya 10:10). Kada ka manta cewa Ibilis yana gazan neman rayukan mutane domin ya sata, ya kashe da kuma hallakad da su, amma Yesu yana son mu (jikinsa) ta

samu wannan madawaniyar rai zuwa dukan mutane ko'ina yana juye kowance halita ya zama sabon halitta! Ubangiji bai ce duka zasu ji su karbi ceto ba, son sa ne domin dukan mutane su sami sira su zo ga sanin gaskiya (1Tim 2:4), amma ya danganta da ra'ayin mutum da zabin sa kuma. Amma Yesu yace dole ne dukan mutane su ji Bishara kafin ya sake dawowa a cikin duniya (Matt 24:14, Markus 16:15, Ayukan Manzani 1:8). Wani ya yi furci mai kyau cewa, "Nasara cikin Bishara shine gayawa wani gama da Kristi cikin ikon Ruhu mai Tsarki da bar ma Allah sakamakon! Aikin mu shine muyi wa'azi amma aikin Allah ya kawo sakamako. "Idan zamu iya sa dukan du-niya ta ji bisharan nan ayau, Yesu zai dawo yau ken-an. Idan kowane Krista a cikin duniya duka ya yi kudurin yin wa'azi akalla ga mutum guda wanda bai tabba jin bishara ba na Yesu Kristi, kowace rana a cikin mako daya, sai Yesu zai dawo war hakka acikin mako mai zuwa. Yana jiran mu! Dawowan Yesu Kristi tana da danganta-ka da yin shelar Bisharan na mulkin Allah. "Wannan Bishara na mulki za ayi wa'azinta a ko'ina cikin dukan duniya domin sheda ga dukan al'umai, kana sai Matuka ta zo" (Matt 24:14). Ka tuna a wancan babban rana lokacin da zamu tsaya agaban sawayen Ubangiji, abin da ya wajaba shine nasara da muka yi domin sunar sa acikin duniya babu abin da ya fihaka! Ka roke Uba a cikin sunar Yesu Kristi domin ya wanke ka ya baka sabowar marmarida juyayi ga battatu, ya kuma baka dabara yadda zakka ribato battatu koda menene za ka biya kamar tamanin yin hakka domin Yesu. Amin.

*"sai suka cewa juna bamu kyautataba wannan rana, ranarce ta albishiri, kuma mun yi shuru idan mun jira har gari ta waye, wani abu mafi muni zai iya faru da mu: ku tashi yanzu mu je mun fada wannan labara a gidan sarki."* ~2Sarakuna 7:9.

*"…Yayakyan sawayen masu shelar bishara ta salama da suna kawo albishiri mai kyau"* ~Romawa 10:15.

---

Domin karabon irin wadan nan yan takardu domin Bishara, ko kuma kana son koyaswa gama da wa'azin bishara a mako daya domin Ikklisiya ko kuma kungiyar ka … domin bayani sai kaa tuntube mu a :

**LIFE COMMISSION MINISTRY**
+23470-32138935, +23480-59153304
P. O. Box 8272, Anglo-Jos, Plateau State, Nigeria.
www.lifecommission.org / lifecommission@yahoo.com